

DEREK PRINCE
MINISTRIES INTERNATIONAL

Abincin Yini

# Jin Dadin Albarkar

*Yesu ya ɗauki talaucin mu domin mu sami yalwarsa*



Furta Kalmar Allah
Daga Derek Prince

Bari mu dubi jerin la'anoni a cikin Kubawar Shari'a 28. Ka karanta wannan surar gaba ɗaya da kanka, don fahimtar ko kana jin dadin albarka ko kuma kana daurewa da la'ana. Idan mu 'ya'yan Allah ne da aka fanshe mu, la'anonin nan ba namu ba ne, amma albarkun ne. Bari mu mai da hankali musamman kan waɗannan albarku da la'anoni da suka shafi wadata da talauci:

> "Amma idan ba ka saurara ga muryar Ubangiji Allahnka ba, da zaka kiyaye dukan dokokinsa da farillansa waɗanda na umurce ka yau, waɗannan la'anoni duka za su auko maka, su tarshe ka:... Da kwandonka da makwaban kullinka zasu zama la'antattu... za ka yi lalaɓe da tsakar rana, kamar yadda makafi ke lalaɓe cikin duhu kuma ba za ka yi albarka cikin tasarrufinka ba... domin ba ka bauta wa Ubangiji Allahnku da farin ciki da dadin zuciya ba, sabili da albarkar abu duka, domin wannan za ka bauta wa abokan gabanka, waɗanda Ubangiji za ya aike maka da su, cikin yunwa da ƙishi, da huntanci da rashin kowanne abu; za ya ɗamrawa wuyanka ƙangi na ƙarfe har za ya hallaka ka." (Kubawar Shari'a 28:15, 17, 29, 47–48)

An bayyana nufin Allah a aya ta 47—cewa mu bauta wa Ubangiji Allahnmu da murna da dadin zuciya saboda yalwar dukan abubuwa. Yalwa kalma ce mai kyau wadda ta bayyana sau da yawa a cikin Littafi Mai Tsarki. Ma'ana, tana nufin samun dukan abin da kake buƙata, da waɗansu—har ma kana da sauran albarku domin wasu. Nufin Allah shi ne mu, a matsayinmu na mutanensa, mu bauta ma Sa da murna da farin ciki saboda yalwar dukan abubuwan da Ya ba mu.

Na gode maka, Yesu, saboda aikinka a kan gicciye. Ina furta cewa zan bauta maka da murna da farin ciki saboda yalwar dukan abubuwa, saboda Yesu ya ɗauki talauci na domin in sami yalwar Sa. Amin.


© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.

**Abincin Yini** ★

Kwafi: WD-B097-133-HAU

Sabuntawa ta ƙarshe: 09 Sept 2026

Yanar Gizo: Derekprince.com/ha/resources




© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.